# DEUTSCHE WELLE
# JI KA KARU

## Kwallon ƙafa salon Afirka
## Kashi na bakwai: Ka bugi ƙwallo ba maƙwabcinka ba

Wanda ya rubuta: Chrispin Mwakideu
Wanda ya tace: Ludger Schadomsky da Maja Braun
Wanda ya fassara: Yusuf Idris

**'Yan Wasa:**

| | |
|---|---|
| Safina: | 'yar shekara 13 |
| Anti Lily: | 'yar shekara 33 |
| Metogba: | ɗan shekara 28 |
| John: | ɗan shekara 15 |
| Shehu: | ɗan shekara 14 |
| Honourable Gambo: | ɗan shekara 55 |
| Zakari: | ɗan shekara 14 |
| Insifeto: | ɗan shekara 40 |
| Mr. Madu: | ɗan shekara 54 |
| Shugaba: | ɗan shekara 67 |

**MAI GABATARWA:**

Masu sauraronmu, barkanmu da warhaka da kuma sake kasancewa da ku a cikin wani sabon shiri na “Ji Ka Karu” wanda muke kawo muku a kan harkar wasan ƙwallon ƙafa a Afirka**.** A shirin da ya gabata, kun ji yadda jami’an ’yan sanda suka zo har filin wasa, suka kama Zakari bisa zarginshi da fasa shagon “Shah Electronics”, inda aka ce ya saci kayan da ke shagon. Tun da farko dai, Anti Lily ta kori Safina daga gidanta, wadda a halin da ake ciki ba ta da wurin zuwa. Sannan shi kuma ƙwararren ɗan wasan nan, Metogba, ya yi roƙo ne a kafafen yaɗa labarai, da cewa iyaye su bar ’ya’yansu, maza da mata, da ke garin Gabas su cim ma burin da suka sa a gaba. Wane irin sakamako wannan roƙo nashi zai haifar? Za a kama Zakari da laifin da ake zarginshi da shi kuwa? Sai ku kasance da mu a cikin shirin na yau domin jin yadda za a ci gaba. Da farko dai za mu fara ne daga gidan Anti Lily. Ta yi wani baƙo da ba ta taɓa gani ba.

**Fitowa ta 1: A gidan Anti Lily**

Safina, Metogba, Anti Lily

**ANTI LILY:** Wane ne? Ina zuwa don Allah.

**METOGBA:** Sunana Metogba. Don Allah ina son in yi magana da ke ne.

**ANTI LILY:** Metogba? To ai ni ban san ka ba. Ka yi haƙuri, ba na magana da baƙi.

**METOGBA:** Da ma maganar a kan ’yarki ne, Safina.

**ANTI LILY:** Wani abu ya same ta ne? Don Allah ka ce min ba abin da ya same ta. Ina take? Na damu ƙwarai a kanta, tun da ta...

**METOGBA:** Ki kwantar da hankalinki, lafiyarta ƙalau. Safina! Hawo sama!

**SAFINA:** To, ga ni nan zuwa. … Sannu Anti Lily.

**ANTI LILY:** Yauwa Safina! Na yi murna da ganinki.

**METOGBA:** Safina ta faɗa min abin da ya faru. Af! Kar in manta, ni ne mai koya mata wasan ƙwallon ƙafa. Na zo ne domin in roƙe ki, ki yi haƙuri ki ƙyale ta ta dawo gida, kuma ki bar ta ta ci gaba da wasan ƙwallon ƙafa. Tana da basira sosai, kuma tana son wasan sosai. Da yake tana ɗaya daga cikin yara mata da suke zuwa wurin gasar, ina ba ki shawarar cewa ki ba ta goyon baya, kuma ki ƙarfafa mata gwiwa.

**ANTI LILY:** Safina 'yata, na yi matuƙar fushi da ke saboda kin ƙi bin umurnina, wannan shi ya tunzura ni har na kore ki. Amma nan da nan na gane kuskuren da na yi, wanda ya jefa ni cikin damuwa a kanki. Kuma idan dai abin da wannan mutumin yake faɗa gaskiya ne, to na ba ki goyon bayana ɗari bisa ɗari! Allah ya ba da sa'a!

**METOGBA:** Kin gani ko, da ma na gaya miki, Safina. In aka tsaya aka yi magana shi ke nan. Yanzu an warware matsala ɗaya. Saura kuma in gano abin da ya sami Zakari.

**ANTI LILY:** Zakari? Me ya same shi?

**SAFINA:** 'Yan sanda ne suka kama shi a filin wasa yau. Suna zarginshi da cewa ya fasa shagon "Shah Electronics". An sace wasu kaya a shagon. Amma na gaya wa Metogba cewa hakan ba gaskiya ba ne, saboda ina tare da shi da yammacin ranar, lokacin da muka taimake ki, bayan kin...kin... uhm…Kin tuna?

**METOGBA:** Na yarda da maganarta. Ban daɗe da sanin Zakari ba, amma

ba na tsammanin zai aikata irin wannan mummunan aiki. Ni ina ganin cewa yaro ne mai tarbiyya wanda idan ya sami dama zai canza rayuwarsa.

**ANTI LILY:** Allah sarki! Ya kamata… Kun ga, ku zo mu je, ya kamata mu taimake shi. Lokaci ya yi da za mu yaƙi rashin gaskiya.

**MAI GABATARWA:**
A yayin da su uku suke shirin tafiya caji-ofis inda ake tsare da Zakari ana yi mashi tambayoyi, a can gidan Honourable Gambo kuwa, John yana cikin nishaɗi ne, yana sauraron waƙe-waƙe, lokacin ne kuma sai wayar gidan ta fara bugawa. Saboda a gajiye yake, sai John ya ƙyale wayar ta yi ta bugawa har…

**Fitowa ta 2: A gidan Honourable Gambo**
Shehu, John, Honourable Gambo

**MURYAR HON. GAMBO (a waya):** Ka buga lambar wayar gidan Honourable Gambo, ɗan majalisarka. Ba na gida a yanzu. Amma kana iya barin sunanka da lambar, ni kuma zan kira ka in na dawo. Na gode.

**SHEHU:** Honourable Gambo, Shehu ne ke magana. Har yanzu ba ni da layin waya, amma na san na kusa samu. An gama kome. An kama Zakari yau. Kuma har yanzu talabijin ɗin da na kwaso daga shagon suna wurina. Ka gaya min lokaci da inda zan same ka, don in karɓi sauran kuɗin. Ka yi daidai yallaɓai. Sai an jima.

**JOHN:** A'a! Me na ji haka! Ba dai mahaifina ba, ba dai Shehu ba. Wannan mafarki ne! Me ya sa? Me ya sa?...

**MAI GABATARWA**:
Jin labarin cewa mahaifinshi ya haɗa baki da abokin Zakari ta hanyar ba shi abokin, wato Shehu, kuɗi don a yi wa Zakari ƙazafi, ya ɗaure wa John kai matuƙa, ya kasa yarda da abin da ya ji yanzun nan. Yanzu zai iya fuskantar mahaifinshi kuwa, ko kuwa zai yanke shawarar ya yi shiru, saboda yanzu tun da an kama Zakari an kautar da mutum ɗaya ke nan daga cikin masu yin gasa da shi? A halin da ake ciki kuma, a can caji-ofis…

**Fitowa ta 3: A caji-ofis**
Zakari, Safina, Metogba, Anti Lily, Insifeto

**ANTI LILY:** Sannu da aiki, Insifeto, mun zo ne mu ga wani yaro. Sunanshi Zaks…Zakari. Da yana…

**INSIFETO:** Kuna nufin sanannen ɓarawon talabijin ɗin nan? Ku biyo ni.

**ZAKARI:** Safina! Metogba! Na ji daɗi kun zo ku gan ni. Ashe har da Anti Lily.

**INSIFETO:** Na ba ku minti biyar, kuma kar ku wuce haka.

**ZAKARI:** Ba bin da na aikata, wallahi ban aikata kome ba. Wannan kuskure ne. Ina kallon TV a wurin, kuma mutane da yawa ma na kallo. Amma dai a wannan yammacin, ina tare da…

**METOGBA:** Mun sani, ba ka aikata ba, Zakari. Muna neman shaidar da za mu nuna haka ne kawai. Kuma ka san in ba shaida, zai yi wuya mu iya fitar da kai daga nan.

**ANTI LILY:** Ka yi haƙuri! Ka yi haƙuri, Zakari!

**SAFINA:** Anti, don Allah ki daina kuka!

**ANTI LILY:** Ba wanda ya gane a cikinku. Dukkanku!

**METOGBA:** Zakari, kana ɗaya daga cikin ƙwarrarun 'yan wasa a wurin gasarmu, kuma ba za mu ji daɗi ba idan muka rasa ka.

**INSIFETO:** Lokacinku ya yi fa!

**ANTI LILY:** Ba mu minti biyar ka ce ka ba mu ba?

**INSIFETO:** E, amma a cikin nan, hakan na nufin minta biyu da rabi ke nan.

**MAI GABATARWA:**
Wannan haɗuwa tsakanin Anti Lily da Zakari ta bar tambayoyi masu yawa a zuciyar Zakari. Me ya sa take kuka sosai haka? Tana tausaya mishi ne kawai? Ko kuwa dai akwai wani abu ne? A yayin da Zaks yake cikin kogin tunani a kan wannan, shi kuwa John yana can gida yana jiran mahaifinshi ya dawo. Bari mu kasance tare da su don mu ji abin da zai wakana.

**Fitowa ta 4: A gidan Hon. Gambo**
Honourable Gambo, John

**HON. GAMBO:** John, yaya kake? Yaya gasar taku take tafiya?

**JOHN:** Lafiya kau. Kana da saƙo a waya.

**HON. GAMBO:** Yaya kake haka, sai ka ce wanda ya haɗiyi ƙwai?

**JOHN:** Da wannan ne ma da ya fi sauƙi, idan na haɗa da abin da na ji a wayar.

**HON. GAMBO:** A'a! Wai, me ke damunka ne? Wane ne ya kira?

**MAI GABATARWA:**
Da ma dai an ce ramin ƙarya ƙurarre ne, kamar yadda ta ƙure wa Honourable Gambo. Amma yanzu me zai faru? Shin John zai iya samun ƙarfin zuciyar da zai tsaya wa gaskiya kome ɗacinta, ko da kuwa zai zubar da mutuncin mahaifinsa? Wan shekare a wurin da gasar take gudana, Metogba bai shirya wa abin da ke tafe ba.

**Fitowa ta 5: A babban filin wasa**
Metogba, Insifeto, Shugaba

**METOGBA:** A yi shiru! Na ce kowa ya yi shiru! Ya yi daidai! Wai! Ban sa ran zan gan ku da yawa haka ba. Ina ganin kamar roƙon da na yi ya yi aiki. To yanzu, da farko zan kasa ku gida gida. Sannan sai mu fara *training*. … Yanzu kuma mene ne Mr. Madu, wai laifi ne a yi wasan ƙwallo a nan ƙasar, ko mene ne?

**MR. MADU:** Ba 'yan sanda ba ne kawai. Metogba, wannan jerin gwanon motocin na shugaban ƙasa ne! Ka yi abin da suka ce ka yi kawai. Sai ka zauna lafiya.

**INSIFETO:** Kowa ya ja da baya! E, kowa da kowa, a ja da baya. Shugaban ƙasa na so ya yi wa jama'ar ƙasa jawabi daga wurin da ake gudanar da gasar nan.

**SHUGABA:** Jama'ar wannan ƙasa, na sami kyakkyawan labarin cewa, an sako ɗaruruwan yara da da can suke yaƙar gwamnatina. Waɗanda wasu daga cikin suna nan filin ƙwallon ƙafa. Kuma na jinjina wa gwamnatina bisa wannan ƙoƙari da ta yi. Wannan abu ne mai kyau ga wannan ƙasa tamu saboda

maimakon a ce yara na ta harbin 'yan'uwansu, yanzu za su koma suna harba ƙwallo a cikin raga. Gwamnatina za ta yi dukkan abin da ya dace don ganin cewa, an bunƙasa wasannin motsa jiki. Za mu shiga gasar neman ɗaukar nauyin gasar ƙwallon ƙafa na cin kofin nahiyar Afirka wanda za a yi nan gaba, kuma za mu samu nasara. Za mu gina sabbin hanyoyi, sabbin filayen wasanni na zamani kamar yadda ake da su a ƙasashen Turai. Sannan kuma matasa za su samu aikin yi. Saboda haka, ba tare da ɓata wani lokaci ba, yanzu na buɗe wannan gasa ta zaɓen 'yan wasa. Na gode.

**MAI GABATARWA:**

Da wannan shewa daga filin wasan ne kuma, muka kawo ƙarshen wannan shiri na yau. Sai mu tari shiri na gaba, don jin abin da John ya ƙulli aniyar yi. Wai shin za a kai Zakari kotu ne, ko kuwa za a kai shi gidan horas da yara ne? Me Metogba ya ƙuduri aniyar yi, bayan shugaban ƙasar ya zo ya shige masa gaba, a wurin da yake gudanar da gasarsa ba tare da wata sanarwa ba? Idan kuna son amsoshin waɗannan tambayoyi, sai ku kasance tare da mu a shiri na gaba. Ana iya ziyartar adireshinmu na yanar gizo domin sake sauraro ko kuma aiko da tsokaci. Adireshin dai shi ne: www.dw-world.de/lbe.